# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**



# ‘Yan Mayakan Gideyon


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**



**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**






**Bayan da Yoshuwa ya mutu, duka mutanen Isra’ila suka yi wa Allah rashin biyayya suka cire shi daga cikin rayuwarsu. Sai Allah ya bar makwabtansu**

**Midiyawa suka kokkone hatsinsu da gidajensu. Sai Isra’ilawa suka koma da zama a kwoguna.**



Wani mutumin Isra’ila, Gideyon, dole ya zama yana da wani wuri a boye inda ya shuka alkama. Sai ya yi girbi ya kuma gyara hatsinsa a wani wurin matse yayan inabi a boye, a karkashi wani babban itace. Midiyawa ba su san wurin ba – amma Allah ya sani! Allah ya aika Mala’ika da sako zuwa wurin Gideyon.

3

Allah ya so Gideyon ya halakar da siffofin allolin karya na babansa sai ya gina bagade ga Allah na gaske. Ko da yake Gideyon yana tsoron mutanen kasarsa domin za su kashe shi, amma duk da haka ya yi abin da Allah ya umarta.



4

Allah kuma ya so Gideyon ya jagoranci sojojin Isra’ila domin su yake mugaye Midiyanawa. Amma Gideyon yana jin tsoro. Sai ya roki Allah wata alama na musamman ya sani cewa Allah yana tare da shi. Sai ya shimfida wani tsumma kamar tabarma mai suman tumaki a kasa.



5



“Idan akwai raba a kan tsumman kadai, kuma kasa yana nan a bushe ko’ina,” Gideyon ya yi addu’a, “to, zan sani cewa za ka cece Isra’ila ta hannu na, kamar yadda ka ce.” Da safe, kasar tana a bushe, amma TSUMMAN YANA A JIKE!

6



Duk da haka Gideyon ya yi shakka. Yanzu yana so Allah ya aika da raban a kasa ba a kan tsumman ba. Washegari – kasar ta jiku, amma TSUMAN YANA NAN A BUSHE!

7

Gideyon ya fara fita da sojoji dubu talatin da buyi (32,000). Allah ya rage su zuwa maza dari uku (300). Allah bai so Isra’ila ta ce “Hannu na ne ya cece ni.” Allah ne kadai Mai Ceton Isra’ila.




8

Cikin sani cewa Gideyon yana jin tsoro har yanzu, Allah ya bar shi ya ji tattaunawa tsakanin wani soja na Midiyanawa da dan'uwansa soja game da mugun mafarkin da ya yi. A cikin mafarkin, ya ga wani burodi yana gangarowa har tentin Midiyanawa har ya rushe tentin.



9

Dayan sojan ya ji tsoro. "Wannan shi ne… takobin Gideyon...," ya yi kuka. Sa'ad da Gideyon ya ji mafarkin da ma'anarsa, ya sani cewa Allah zai ba shi nasara.



10

Gideyon ya shirya harin dare. Ya ba wa kowane soja kaho, da sanda mai rami da wuta a ciki. Sai suka kewaye sojojin Midiyanawa.



11

Da Gideyon ya ba da alama, sai sojojin suka hura kahoninsu, suka faffashe sandunansu suka kunna wuta. Ina misalin surutu! Sai ga rikicewa! Sai Midiyanawan da suke tsoro suka tashi suka gudu.



12

Bayan wannan babban nasara, mazan Isra'ila suka ce wa Gideyon ya yi mulki a kansu. "Ba zan yi mulki a kan ku ba… UBANGIJI ne zai yi mulki a kanku." Gideyon ya amsa musu. Ya sani cewa Allah ne kadai yake da 'yanci ya yi mulki a kan rayuwar mutane.



13

'Yan Mayakan Gideyon

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Alkalai 6-8

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

14

# KARSHE

15

60



Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da
Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16